# Salon Hausar Mata Hausawa

Abdullahi Lawal Dikko


## Tsakure

Wannan Maƙala wani fage ne na nazarin ilimin walwalar harshe, bincike ya ta'allaƙa ne a kan tausasa murya a maganar matan Hausawa. An yi tsokaci game da ma'anar magana da tausasa murya, kuma aka zayyana yadda ake samun Hausar mata zalla. Sannan an taskace ayyukan da suka gabata a kan mata. Nazarin binciken ya gano cewa akwai wasu kalmomi da suka ta'alaƙa ga mata, kuma mata na da tausasa murya wajen yin magana. Sanadiyyar haka sukan ɗauki tunanin samarinsu ko mazansu ta hanyar hila da rausayar murya irin ta mata.


## 1.0 Gabatarwa

Muradin wannan takarda shi ne a bayyana yadda matan Hausawa ke tausasa murya a wajen maganganunsu na yau da kullum. Lalle mata gwanaye ne wajen tausasa murya da rausaya idan suna Magana tsakaninsu da mata 'yan uwansu ko kuma maza. Kusan ma ana iya bugun ƙirji a ce tausasa murya da hila na mata ya fi ƙarfi in ga maza a gaba gare su, ba domin komai ba sai domin jawo hankali. A wannan takarda an tattara bayanan da suka shafi magana a bakin mata Hausawa, inda aka kawo ma'anar Tausasawa da ma'anar murya da magana, sannan an yi tsokaci a kan abin da ya shafi bambancin maganar mata da maza da bayyana yadda zalaƙar harshe yake a bakin mata da fasahar magana kamar yadda aka taskace su ɗaya bayan ɗaya.

## 1.1 Ma'anar Magana

Magana wajibi ce ga duk wani ɗan Adam mai motsi a doron ƙasa, saboda haka, ya zama dole mutum ya yi magana da ɗan uwansa domin biyan buƙatun yau da kullum. Dangane da ma'anar magana ga abin da aka faɗi cikin Kamusu na CNHN (2006:116)

> "Magana (maganaa, sn, mc, jam, magangannuu ko maganoonii) (i) jerin kalmomi da aka furta da baki, kuma masu ma'ana, d-d kalma ko kalami (ii) jawabi ko batu (iii) faɗa".

Ya kamata a lura cewa, ita magana tana da muhallin yinta da kuma irin yadda ya kamata a yi, sannan cikin magana akwai kunya, domin ba komai ne za a fito gaba gaɗi a faɗi ba, sai an tauna sa'annan a ciza a busa. Misali maganar da za a yi tsakanin surukai dole ta bambanta da wanda ke akasin haka domin akwai surukuta, haka maganan da miji zai yi da matarsa in akwai yaro ko yarinya a wurin dole ya sakaya musamman abubuwan da suka shafi zaman aure da batun soyayyar auren. Lallai in kuwa haka ne kunya wajiba ce wajen furta magana. Bunza (2006:61) ya ce:

> "Hausawa na cewa, wata magana sarakuwar baki ce. Abin nufi a nan,ba kowace magana ake furtawa gaban kowane mutum ba ko a baki kowane mutum ba. Akwai wadda mai faɗa kawai zai ji kunya ba mai sauraro ba. Akwai wadda mai sauraro kawai zai ji kunya ba mai faɗa ba."

Dangane da Batun yanayin magana kuwa Yakasai (2012:64) ya tabbatar da cewa:

"Magana takan zamo dole ko wajibi a wajen Bahaushe yayin da ya sami kansa a cikin ɗaya daga cikin waɗannan yanaye-yanaye:

i. **Hani da Horo:** Al'amuran da suka shafi koyarwa na addini ba su buƙatar a sakaya su, dole ne a bayyana su yadda suke domin manufar da maƙasudin saƙon ya zama ya isa daidai. Babu kunya a cikin koyarwa na addini, ana buƙatar a fayyace komai dalla-dalla.

ii. **Kariyar kai Daga Zargi:** Wajibi ne ga kowace jinsin al'umma ya zama sun kare kansu daga duk wani zargi don gudun kar mutuncinsu ya faɗi a idon al'umma. Hausawa na cewa "Mutunci madara ne, in ya zube ba ya kwasuwa." Saboda haka ya zama wajibi ga mace ko namiji su kare kansu daga duk wani zargi da ake samu a kowane yanayi batare da jin kunya ba.

iii. **Al'amuran jama'a:** Batun da ya shafi jama'a, wajibi ne a fito fili a bayyanar batare da an sakaya ba ko jin kunya ba. Duk jama'ar da ke ƙaunar cigaban al'umma ta fuskar al'amuran da suka shafi rayuwar yau da gobe na buƙatar shiryatarwa zuwa ga ayyukan ƙwarai babu ɓoyo, kuma ba kwana a ciki.

### 1.2 Ma'anar Tausasa

Batun kalmar tausasa ba sabon abu ne ba a harshen Hausa, da kuma yin mu'amula da kalmar cikin zamantakewar Hausawa. Sai dai kuma ana amfani da kalmar a Hausa ta fuskoki mabambanta, ya danganata da irin saƙon da za a isar da muhallin da za a yi amfani da shi cikin zantukan da za a yi. A cikin Kamusun Hausa shafi na 434 an fassara tausasa da cewa:

> "rausasa, mis: ta-murya (i) sassauta, mis: ya- murya (ii) yin tausayi,mis: ya –wa al'amajiri"

Saboda haka a nan mu na iya ɗaukan sa da ma'anoni biyu. Na farko mai alaƙa da murya domin yin ƙasa da ita. Na biyu kuwa jin tausayin na ƙasa da mutum, misali, almajiri da mai naƙasa. Amma mu a nan batun tausasa murya da mata ke yi muke nufi kamar yadda ya zo a misalai na sassauta da rausasa murya a bakin mata.

## 2.0 Ayyukan da suka Gabata

An sami masana da manazarta da suka gabatar da bincike dangane da al'ammuran da suka shafi mata a batun harshe da dama, ta fuskoki mabambanta, musamman abin da ya ta'allaƙa kan yadda ake amfani da harshe a Hausa da kuma irin danniyar da ake ganin maza na yi wa mata. Wannan al'amari ya ƙara samun gindin zama a duniya baki ɗaya ba ma a Nijeriya ta Arewa ko ƙasar Hausa ba. Wannan na da nasaba da taron duniya kan `yanci mata da ƙananan yara na birnin Beijin na ƙasar Sin. Taron ƙara assasa bincike da neman matsayi game da mata a dukkanin al'ammurorin rayuwa ta yau da kullum. Wani abun burgewa shi ne, su kan su matan ba a bar su a baya ba, wajen bayyana ra'ayinsu.Misali, masana da manazarta irinsu Lakoff (1975) Augi (2000), Ibrahim (2002)

Muhammed (2007),Muhammed A (2007) Majid (2012) duk sun gabatar da ayyuka a wannan fage na ilimi, ga abin da kowannensu ke faɗi.

Lakoff (1975) ya yi mashi sharhi ne game da fahimatar harshen da mata ke amfani da shi a tsakanin masu magana da harshen ingilishi. Ya yi ƙoƙarin haskaka launi da bayyana matsayinsa ta fuskar mace, sa'annan aka yi yunƙurin tattara bayanai na abubuwa daban-daban. Haka kuma, an nuna matsayinsu a harshe ta hanyar yin tambayoyi. Misali: Siffantau, kalmomin launi, hawa da sauka da ake samu a cikin jumloli na magana da nusar da yin tambaya kaikaice da kuma maganganun da suka jibanci girmamawa a tsakanin al'umma.The virtuous Woman" zuwa Hausa Wanda aka fassara da "Mace Ta Gari" a ciki ta yi sharhi game da ma'anar Fassara da manufarta, da siffofinta, tare da bayyana muhimmancin fassara, inda ta nusar da mu muhimmancin fassara a wajen neman ilimi, sannan kuma a halin yau ana ta gwagwarmaya a kan neman ilimin mata da bayyana muhimmancinsa a cikin rayuwa ta yau da kullum. Ibrahim (2002) kuwa an ba da gudummuwa ne a kan tarke ayyukan labarai na Alƙalai, a inda ta yi tsokaci dangane da shuru-shura na al'adun mata inda aka ankarar da cewa mata kan kasance shuru musamman gaban surukansu, ba su faye yin magana ba. Sakamakon nuna girmamawa, duk da cewa akwai tasirin Musulunci wajen yin biyayya da yin shuru da kamewa a gaban na gaba ta ita. A Muhammed (2007) an bayyana matsayin mace da kimarta a cikin al'ummar Hausawa, aka kuma bayyana sauye-sauyen da ake samu sakamakon rubuce-rubuce da ake yi dangane da mata a harkokin yau da kullum, ta fuskar ƙagaggun labaru.

Har wa yau, Muhammed (2007) an taskace al'ammuran da suka shafi lamarin jinsi, kamar yadda ake tauye haƙƙoƙin `yan mata a cikin zamantakewar al'umma, inda aka bayyana cewa iyaye mata su ne ƙashin bayan duk wani danne haƙƙoƙin yara mata. Manazarciyar ta zayyana irin alaƙar da ke aukuwa, tana mai bayyana halayyar da ake samu a wajen zamantakewar mata. Misali kamar abubuwan da suka shafi 'yancin mata. Nuna fifiko a tsakanin maza da mata. Da ɗaukan da ake yi cewa maza sun fi mata ƙoƙari, sannan da matsayin da maza ke ɗauka wajen jagoranci a gidaje. Majid (2012) kuwa an yi sharhi ne game da al'ammuran da ke aukawa a yau dangane da mata, ta bayyana matsayinsu ta fuskar addini, al'adu, siyasa ilimi, sa'annan ta bayyana irin yadda maza ke ɗaukarsu a matsayin marasa ƙarfi ta kowane fanni duk da cewa sun fi kowa yawa a duniya, amma ba su isa su sa a ji sba. Ta yi ƙoƙarin yin inkari a kan waɗannan batutuwa.

Sokoto (2012) da Rabi (2012) sun yi batu a kana bin da ya shafi magana dangane da mata ga abin da suke cewa: Sokoto (2012:364) ya nusar a kan abubuwan da suka shafi salon sarrafa harshe a cikin rubutacciyar waƙar soyayya ta Hajiya Hauwa'u Kulu. Ga abin da yake faɗi:

> "Dangane da kalmomin fannu, Hajiya Kulu ta yi amfani da su a wurare da dama a cikin waƙarta, domin kowane fanni na ilimi yana da nasa kalmomin da suka keɓanta da shi, kamar a ce abin da ya shafi aikin gona ko na likita ko na siyasa ko na kimiyya da sauransu. To da yake fannin da Hajiya ta wallafa waƙartaa kai shi ne soyayya, sai aka sami kalmomi masu yawa waɗanda suka danganci wannan fannin. Misali an sami kalmomi irin su farin jini da sahibi da aure da kyawo da biyayya da sauransu."

Ita kuwa Rabi (2012:387) ta yi bayanin irin abubuwan da mace ke magana ne a cikin zuciyarsu, inda ta bayyana mana:

> Matan Hausawa na amfani da waƙa ne, wajen fito da abin da ke cikin zuciyarsu ne saboda yanayin al'ada da addini domin ba komai ne suke iya faɗi ba, saboda kunya. Har ila yau, kamar yadda aka sani, mace halitta ce mai rauni, idan aka kwatanta ta da namiji musamman a ƙasar Hausa, domin ba su iya fitowa fili su bayyana matsalolinsu. Wannan ne ya sa wannan binciken ya fayyace yadda matan Hausawa ke nuna takaicinsa da fito da shi sarari ta hanyar waƙar baka. Irin wannan takaici ya haɗa da kishi da kunya da matsalar zaman auren dole da matsalar kayan ɗaki da haihuwa.

## 3.0 Bambancin Maganar Mata da ta Maza

Mata sun kasance ma'abuta shirya duk wani zance da za su gabatar ko furta kafin su faɗi. Suna amfani da basira da tunani da natsuwa da hazaƙa da nuna ƙwarewa wajen tsara zantukansu na yau da kullum. Idan muka yi la'akari da abubuwa huɗun da muka zayyana da mata ke amfani da su wajen shirya zance wato:

a. basira b. tunani

c. natsuwa d. hazaƙa

Da farko mun tabbatar da cewa maza da mata na amfani da harshe wajen hulɗa na yau da kullum, domin haka babu tababa dole a sami ƙwarewa ta fuskar amfani da harshe.

Har wa yau, sakamakon hulɗa da ake yi ana samun karuruwan harshe mabambanta. Sa'annan kuma mata na kasancewa masu zaɓen kalmomin da za su yi amfani da su wajen yin magana. Sakamakon tausasa murya da yin magana diƙin-diƙin ya haifar da samuwar zaɓen kalmomi masu jawo hankali da kuma yin amfani da kalmomi na saye da sara domin sirrintawa a tsakaninsu da juna.

Yakasai (2007:97) ya haskaka dangane da bambancin da ake samu na harshe tsakanin mata da maza. Ga abin da yake cewa:

> Bambance-bambance da ake samu a harshe yana faruwa ne a sanadiyyar irin halayyar da al'umma ke nunawa ga mata. A waɗansu al'ummu maza da mata na amfani da harshe wajen hulɗa tare, ba da an sami wani cikas ba. A irin wannan yanayi ba a sa ran samun wani tasiri na a –zo-a-gani. Amma kuma a wasu al'ummu, sadarwa tsakanin maza da mata a takure take ta yadda sakamakon hakan na bayyana a al'amura na zamantakew da kuma na magana ko da yake akwai bambance –bambance a tsakanin maza da mata a magana, ko 'yan bambance-bambancen kawai na zaɓin amfani da kalmomi a yanayin da suka dace,lallai dai suna amfani ne da karuruwa daban-daban na harshe guda.

Harshe a matsayinsa na furuci mai ma'ana da fa'ida shi ne mata ke sarrafawa cikin magana domin isar da saƙo cikin zukatansu na al'amuran da suka danganci rayuwarsu ta yau da kullum. Mata sun taimaka wajen bunƙasa harshe ta hanyar faɗaɗa ma'anar kalmomi cikin hikima da fasaha da

niyyar jawo hankalin samarinsu kan irin soyayyar da suke da itagare su, ta hanyar yin sara. Yawanci sukan Tausasa murya idan sun zo faɗi. Ga irin furucin da suke furtawa a matsayin misalai:

| Kalma | Ma'ana |
|---|---|
| Mai Martaba | Saurayi da ake so |
| Na ƙarfe | Saurayin da za a aura |
| Dodo | Saurayi |

A lokacin da mace take daka ta fara lugude ta na zagin kishiyarta ko wata maƙwabciyarta, ita ma wacce ake da itan ta sani, sai ta ɗauko turmi ta mai da martani wato ta rama. Misalin Habaicin da mata kan yi a lokacin daka shi ne:

"Durƙusa ki auna man 'yar ganin ƙwafi.

Da ke na nuna mana kin ji daɗi

Amma yanzu mu ka auna maki kun ji haushi.

Bankaɗaɗɗa ma sha lawar rahaina

Ba wanka ke ce wani ba shi wanka".

Habaicin da mata kan yi a dutse (wato) lokacin yin niƙa sun haɗa da:

Kin ce ubanki ba ya sata,

ke kika ce ubanki ba ya sata.

Tun daga nesa na ji ihu! Ihu !

Ubanki ya saci ƙashin miya!

A taƙaice, duakkan waɗannan bayanai na nunan irin salo da mata ke amfani da su wajen magana.

Ɗalhat (2002:12) ya bayyana cewa mata su ne ake ganin sun fi kowa yin habaici kamar haka: "Habaici ba ya zuwa sai bayan auwakuwar sanadin yin sa ya faru. Misali sau da yawa in mutum

ya je ya sami mutane musamman mata waɗanda ake ganin su suka fi kowa yin habaici ya ce su faɗa masa duk irin habaicin da suka sani, mafi yawan lokuta sai ka ga sun kasa."

Saboda haka, za mu iske cewa duk waɗannan Habaici ne da mata ke yi. Ana kyautata zatun cewa mata ne suka fi amfani da Habaici, kuma habaicin wanda take ratsa zukata in har ta fito, Na farko ga ƙona zuciya, na biyu ta fito cikin tausasa murya da rausaya don dai ta ɓata zuciyar wanda ake ma, musamman ma kishiya. Dalhat (2002) ya yi sharhi dangane da habaici a bakin matan Hausawa ga abin da yake cewa:

> Mata waɗanda ba kishiyoyin juna ba ma na ma junansu habaici, kamar misali, matan gidan haya masu maza daban-daban ko kuma in sun haɗu kuma makamantansu, saboda ma dai a nuna cewa mata ƙwararru ne wajen yin habaici mace kan zagi kishiyarta ko wata maƙwabciyarta a turmi in tana daka ko a dutsen niƙa idan tana niƙa haka kawai ma mace kan ɗauki taɓarya ko ba za ta daka komai ba ta sa a turmi ta raira su cikin murya na musamman da tausasawa da yin rausaya dan kishiya ta ji haushi"

Har wa yau akwai wasu habaice-habaice da mata ke amfani da su kamar haka:

A yi can dai Umma ta gaida A'isha

A tafi dai Bora ta yi yaji

Ba kuka na ba, Uwar kishiya ta mutu.

Galibi, salon da mata ke amfani da shi wajen aiwatar da magana ya sha bamban da na maza. Domin mata Allah ya hore masu wata murya ta musamman wadda ta tabbatar da cewa lalle su mata ne, musamman wajen tausasa murya da fitar ziza, da rausayar murya, da yin amfani da gira, da karya harshe yadda zai jawo hankali mai sauraro tun ma ba a ce ɗa namiji ba. Ga abin da Coates (1986) ke faɗi, kamar yadda na ciro daga Adamu (2008:17).

> The idea that women discusses topic which is essentially trivial has contribute to the myth of Women's verbosity.
>
> Da ana cewa tunani mata sun cika maganganu marasa amfani, shi ya sa ake cewa sun cika surutu.

A lokacin da mata suke magana sukan yi ƙoƙarin tausasa murya da jawo hankali cikin tausasa magana, sanadiyyar haka yakan sa su cim ma burin abin da suke nema a wajen miji ko saurayi. Ba abin mamaki ba ne a ce mata sun fi maza tausasa murya, domin shi namiji mafi yawan lokuta duk wani abu da mace za ta nema a wajen shi take nema, shi ne mai bayarwa, ɗawainiyar su tana kan maza ne.

Dalili shi ne maza akwai su da nuna iko ko fifiko a kan al'amuran da suka shafi mata. Saboda haka, kowane lokaci suna zartar da zantukansu ne cikin iko da nuna isa.

Misalan lafuzzan ɗauke hankali da mata ke amfani da su.

| Kalmomin `Yan mata | Ma'ana |
|---|---|
| i. Rabin rayuwata!(rabin ráyuwáátáá | Surayinta |
| ii. In ba kai ba rijiya!(in ba a kai su, ba sai rijiyáá) | Nuna shagaba ga masoyi |
| iii. Wai ka zalahoto(wai kai zaláháhóótóó) | Zolaya ce 'yan mata kan yi wa mai wahala da ba sa son sa. |

Idan muka duba da idon basira za mu iske cewa na cikin baka a misalan da suka gabata na nuna yadda mata ke tausasa murya ne, wajen jawo hankalin samarinsu, cikin tausasa murya da yin hila, a wani lokaci kuma da nuna zolaya ko `ya`ya (wada kani) duk a gida guda zaune tare da matansu wanda kan haifar. Buga da ƙari, akwai inda mata masu zaman kansu kan ci karensu ba babbaka, sai dai akwai magajiya wanda ita ce shugaba a gidan, nan ma Hausar ta bambanta. Idan muka haɗa waɗannan matakai na mata guda uku, za mu ga lallai duk cika Hausar ta bambanta, amma duk mata ne yanayin zamantakewar da halayar ta sha bamban, sakamakon haka, Hausar dole ta bambanta.

Domin ya zama zakaran gwajin, ga abin da Yakasai (2012;117) ya ce: "Ga dai wasu misalai kaɗan da za mu iya bayarwa daga Hausar `yan mata kamar haka: A taƙaice muna iya cewa babu wani takamaimai fifiko a tsakanin maza da mata wajen amfani da harshe, duk da cewa akwai buƙatar nazartar muhimmancin harshe a halin da muke ciki yau, ba sai gobe ba. Amma in mun yi la'akari da abin da ya shafi jagoranci a cikin al'umma kai tsaye mun san maza su ne jagororin al'amuran yau da gobe, kama tun daga gida har a hukumance. Sai dai Yakasai (2012:91) ya nusar da mu cewa:

> Idan dai ta la'akarii da tsauraran batutuwan harshe ne ya sa ake ɗaukar mata sahun baya cikin mu'amalar sarrafa harshe, to da alama akwai buƙatar tsokaci kan abubuwa guda uku. Na farko dai akwai buƙatar a tantance irin keɓaɓɓun kalmomin da maza ke da fifiko a kai, ta yaya suka mallake su kuma me ya sa hakan yake kawo cikas ga mata? Domin fahimtar waɗannan batutuwa, ana iya mai da hankali kan muhimmancin harshe.

## 4.0 Kammalawa

A cikin wannan takarda an fito da yadda mata ke amfani da harshe domin isar da saƙonni cikin hikima da nuna zalaƙar harshe. Sa'annan an nuna yadda suke tausasa murya a wajen magana tsakaninsu da mazajensu. Binciken ya tabbatar da cewa mata na da lafuzza da kalmomi na musamman da suke amfani da shi wajen sakaya zance, da kuma wasu keɓaɓɓun kalmomi da sukan kira samarinsu da shi, saboda nuna hila ko yaudara. Bugu da ƙari, wannan takarda ta jaddada cewa mata na da zaƙin murya mai laushi da taushi da su ka fi maza.

## Manazarta


Adamu, A.U. (2008) Salon Taɗin Mata Hausawa Ma'aikata a Cikin Garin Kano, Kundin Digiri Na Biyu, Bayero University, Kano. P17

Augi. H.M. (2000) "The Virtuous Woman" " Mace Ta Gari" Kundin Digirin Farko Usmanu Ɗanfodiyo University, Sakkwato P1-11.

Bunza, A.M.(2006) *Gadon Feɗe Al'ada* Wallafar Maɗaba'ar Tiwal Nigeria Ltd. 16 Akinbaruwa Street, Off. Atunrase Street, Surulere, Lagos. P61

CNHN (2006) *Kamusun Hausa* Bayero University Printed By Ahmadu Bello University Press Limited 4 Samaru, Zaria. Nigeria. P116

Dalhat, A.M. (2002) "Habaici da Dangantakarsa Ga Al'ummar Hausawa," Kundin Digiri Na Farko Department of Nigerian Language Usmanu Ɗanfodiyo University, Sokoto.

Garba, R. (2012) "Mace a Bakin Mace: Nazarin Huce Takaicin Matan Hausawa a Waƙoƙinsu." Department of African Languages and Cultures, Faculty of Arts, Zaria. Ahmadu Bello University. P 387 – 400

Ibrahim, R.A. (2002) "Growing Wings' A Feminist Critigue Alkali's Cobwebs and Other Stories" FAIS Journal of Humanities, Vol. 2, No.2 Bayero University, Kano. P277-293

Kabir, B.U. (2004) "Nazari Kan Hausar Mata Matasa A cikin Garin Kano" Kundin Digiri Na Biyu, (M.A. Hausa) Department of Nigerian Langfuage Bayero University, Kano. P1-24

Lakoff, R. (1987), Language and Woman's Place, New York, Harper & Row.

Majid, R.A. (2012) *Mace Mutum*, Ɗab'in Iyaruwa Publishers, Kano No. 6971 Bompai, Kano: Nigeria.

Muhamme, B.S.(2007) "Women Hausa Writers and Social Change." FAIS Journal of Humanities Vo. 3 No.7 November, Bayero University, Kano.

Muhammed, R.T. (2007) "The image of the girl child as aA maternally oppressed individual and her self-appraisal; in *El-Sa'adawi's Memoires of Woman Doctor*. FAIS Journal of Humanities Vol 3 No7.Bayero University, Kano. P 58 – 76

Sokoto, A.H. (2012) "Kallabi Tsakanin Rawuna: Nazari da Sharhi a kan Rubutacciyar Waƙar Soyayya ta Hajiya Hauwa Kulu Champion of Hausa Cikin Hausa A Festschrit in Honour of Ɗalhatu Muhammad. Department of African Languages and Cultures, Faculty of Arts, Zaria. Ahmadu Bello University. P 360 – 363

Yakasai, S.A (2004) "Sadarwa Tsakanin Maza Da Mata: Nazarin Dangantakar Harshe Da Daidaituwar Jinsi."Algaita *Journal of Current Research in Hausa Studies* No3, Vol.1 P89 – 100

Yakasai, S.A. (2012) *Jagoran Ilimin Walwalar Harshe*, Ɗab'in: Gida Mai Lamba 52 Layin Sarki Yahaya. Sokoto – Najeriya. P64 – 117